# DEUTSCHE WELLE
# JI KA KARU

## Kowa dabam Allah ya yi shi: Mutunta haƙƙin tsirarru
## Kashi na goma: Mu cashe rawa – 'yan Afirka a Jamus

Wadda ta rubuta: Marta Barroso
Wanda ya fassara: Ɗanlami Bala Gwammaja
Wadda ta tace: Halima C. Schmaling

**'Yan Wasa:**

Mai ba da labari

Yahi Nestor Gahe: ɗan shekara 32

Steve Bimamisa: ɗan shekara 30

Ɗan wasa: ɗan shekara 30

**Mai gabatarwa:**

Masu saurarenmu, barkanmu da sake kasancewa da ku a cikin kashi na goma kuma na ƙarshe a jerin shirye-shirye da muke kawo muku a kan kare haƙƙin tsirarru mai taken “Kowa Dabam Allah Ya Yi Shi - Mutunta Haƙƙin Tsirarru”. A labarurrukan da muka kawo muku daga sassan nahiyar Afirka, mun kawo muku labaran al’ummomi waɗanda ke fafutukar yaƙi da irin bambancin da ake nuna musu.

A shirin namu na yau, za mu gana ne da waɗansu matasa, wato Nestor da kuma Steve. Dukkansu dai ’yan Afirka ne da ke da zaune a ƙasar Jamus inda kuma suke ƙoƙarin ganin an samu cuɗanya da haƙuri da juna. Wannan shi ne saƙon da suke isarwa a cikin waƙe-waƙe da raye-rayen da suke yi, wato a zauna tare maimakon zaman ’yan marina.

**Mai ba da labari:**

Lallai kam! Nan da awa ɗaya da rabi Nestor Gahe zai hau kan dandamali, amma kuma hankalinsa a kwance, babu wani zulumi. Shi dai wannan matashi yana zaune ne a ƙofar babban wani gini mai suna “tri-bühne” wanda zaure ne na wasannin kwaikwayo da kaɗe-kaɗe da raye-raye da ke garin Stuttgart na ƙasar Jamus. A wannan wuri ne Nestor Gahe yake aiki, a matsayin ɗan wasan kwaikwaiyo da koyar da raye-raye. Yana zantawa ne da wani abokinsa mai suna Steve Bimamisa a lokacin da yake shan shayi. Suna amfani da wannan dama da suke da ita ta wannan ɗan lokacin da suka samu don su tattauna a kan wani sabon wasa da suke aiki a kansa mai suna “Gumboot meets Schuhplatteln”. Saboda lokaci yana ƙaratowa, za a gabatar da wannan wasa ne a cikin wannan gidan wasan kwaikwaiyo na “tri-bühne” nan da watanni biyu masu zuwa. A nan ne Steve ke fatan gabatar da wannan sabon wasa nasu.

**Bayanin Steve cikin Jamusanci:**

*“A wannan wasa namu mun haɗa irin rawar nan da ake yi ne a Afirka ta Kudu mai suna ‘Gumboot’, da kuma irin wadda ake yi a Bavariya mai suna ‘Schuhplattler’. Tsarin shi ne, Nestor zai fara da rawar Gumboot, daga nan*

*kuma sai ya canja ya koma ta Schuhplattler."*

**Mai ba da labari:**

Ita kuwa rawar Schuhplattler, rawa ce ta gargajiya da ake yi a kudancin garin Bavariya na ƙasar Jamus. Samari sun ƙago wannan rawar ne don su dinga burge 'yan mata wajen neman aure. Ita dai wannan rawa ta ƙunshi tsalle ne da wani taku na musamman, kuma idan suna yi suna saka wani wandon fata ne na gargajiya mai suna 'Lederhosen'. Duk da cewa waɗannan raye-raye sun samo asali ne daga nahiyoyi dabam-dabam, amma a wajen makaɗa da mawaƙa akwai kamanceceniya a tsakaninsu. Wannan haɗakar rawa ta Gumboot da ta Schuhplattler ta zamo wa Nestor da Steve wani sabon wasa da suke tinƙaho da shi. Ana kiran wannan ƙungiya tasu da suna 'Diversité'. Kuma kamar yadda 'yan wannan ƙungiya sukan bayyana, wannan wani nau'i ne na hatsin bara da ya game nau'in kiɗan Kasar Turai kamar na 'soul', da na Afirka, wato 'African rumba', da 'afro-beat', da kuma busar 'jazz' da kuma wani nau'i na kaɗe-kaɗen gargajiya. A ganin Nestor, wannan ƙungiya tasu ta 'Diversité', ko kuma 'diversity' da Turanci, ta wuce zancen haɗakar kaɗe-kaɗe da raye-raye.

**Bayanin Nestor cikin Jamusanci:**

*"Kalmar 'diversity' ko kuma 'diversité' na nufin cewa kowane ɗaya daga cikinmu ya sha bambam da ɗan'uwansa. Amma kuma idan muka haɗa kai za mu cimma manufa."*

**Mai ba da labari:**

Wannan ƙungiya dai ta 'Diversité' ta ƙunshi makaɗa da mawaƙa da suka fito daga ƙasashen Afirka da kuma ƙasar Jamus. Suna gabatar da wasannin nasu a tsari dabam-dabam, kuma ya danganta da yanayin wasan. Amma kuma fitattu daga cikinsu su ne mutum ukun nan, wato Nestor da Steve da kuma mawaƙi kuma marubucin waƙoƙi mai suna Michael Dikizeyeko. Dukkansu sun bayyana cewa babu wata hanya ta haɗa kan mutane fiye da hanyar kaɗe-kaɗe da raye-raye ta hanyar amfani da takalman gumboots da kuma wandunan Lederhosen. Wannan a ganin Steve ita ce kyakkyawar hanyar

bayyana dabarunsa na haɗin kai a cikin al’ummar da ta rarraba.

**Bayanin Steve cikin Jamusanci:**

*“Abin da muke nuna wa mutane shi ne, ku duba ku gani yadda kuka bambanta, ga mu baƙaƙe ne mu, amma kuma ga shi mun zo muna taka rawarku ta Schuhplattler.”*

**Mai ba da labari:**

Shi dai Steve ya daɗe a ƙasar Jamus. Ya iso nan ne tare da iyalinsa daga Jamhuriyar Dimukuraɗiyar Congo shekara 16 da suka wuce. Kuma ya samu yin karatunsa ne a wata makaranta da ke kusa da garin Stuttgart. Yanzu shekarunsa na haihuwa sun kai kusan 30, ko da yake dai bai cika son bayyana ainihin shekarunsa ba. Steve dai mutum ne mai azamar kasuwanci. Ya kasance yana shugabantar harkar waƙa na tsawon shekaru shida. Kuma tun daga shekara ta 2009, shi ne yake shugabantar ƙungiyar ‘Diversité’. Shi a wajensa yana ganin ƙasar Jamus na shirin buɗe ƙofarta ga duniya, har ma kuma ga ’yan gudun hijira.

**Bayanin Steve cikin Jamusanci:**

*“Tun daga shekara ta 1998 har zuwa ta 2000 yana da wahala ga duk mutanen da suka zo daga Afirka su samu gidan hayar da za su zauna. Ko’ina muka je sai a hana mu. Duk gidan da muka je, sai a ce an bayar da gidan haya. Amma kuma bayan ’yan sa’o’i biyu, sai mu ga an sa waɗansu a ciki. A lokacin da nake aikin sikawut, nakan zo Garin Stuttgart. A ko da yaushe za ka ga ’yan sanda suna ta farautar ’yan Afirka. Yanzu kam abin ya sauya.”*

**Mai ba da labari:**

A wani bincike da Hukumar Bin Haƙƙin Ɗan Adam ta Tarayyar Turai ta sa aka yi a shekarar 2009, ta gano cewa a cikin Tarayyar Turan akwai wani jinsin mutane da ake kira Roma ko kuma ‘gypsies’ waɗanda su ne aka fi nuna wa wariya daga cikin jinsin da ke Tarayyar ta Turai. Waɗanda suke biye da su kuma su ne ’yan gudun hijira daga kudancin da kuma yammacin Afirka.

Kungiyar dai ta ‘diversité’ ta ɗan fuskanci ’yan matsaloli. Domin kuwa ya

zamar mata wajibi ta saya wa 'yan rawarta wandunan rawar nan na Lederhosen. Wandunan da suka fara saye sun yi tsayi da yawa, na biyun da suka saya kuma suna hana su sakat idan suka zo yin rawa. Dole sai da suka je suka yi cikakken nazarin yadda ake yin rawar ta 'yan Bavariya, sannan kuma suka yi mata 'yar kwaskwarima, kana kuma suka yi ta atusaye.

**Bayanin Steve cikin Jamusanci**:
*"Muna ganin cewa haɗin kai fa batu ne da yake buƙatar dagewa, musamman ma dai ga su 'yan rawar. Mun lura cewa duk lokacin da muka kammala wasa za mu ga cinyoyinsu sun yi shaida, saboda idan ana rawar Schuhplattler ana yi ana dukan cinyoyi. Ni abin yana burge ni, ganin cewa koyon wani abu sabo fa ba sauƙi gare shi ba. Zama tare da juna abu ne da yake da tasa matsalar. Domin kuwa yana buƙatar haƙuri da juriya."*

**Mai ba da labari:**
Ofishin Hukumar Kula da Shige da Fice da kuma Al'amuran 'Yan Gudun Hijira na ƙasar Jamu ya bayyana cewa, a shekara ta 2010 akwai baƙi 'yan ƙasashen waje kusan miliyan bakwai da ke zaune a ƙasar ta Jamus. A yankin Baden-Württemberg inda Nestor da Steve suke da zama, kusan kashi sha ɗaya cikin ɗari na mutanen wurin baƙi ne 'yan ƙasashen waje. Duk da irin waɗannan bayanai da suke fitowa, rahoton binciken da Hukumar Kare Haƙƙin Ɗan Adam ta Tarayyar Turai ya yi a shekarar 2009 na nuni da cewa, har yanzu manufar gwamnatin Jamus ta karɓar baƙi fa a ƙasar ana aiwatar da ita ne rabi da rabi. Wannan ke nan na nufi ƙasar ta Jamus yanzu ita ce ta tsaka-tsaki a tsakanin ƙasashen da ke aiwatar da wannan manufa daga cikin ƙasashen da ke cikin Tarayyar Turai.
Shi dai Nestor ya zo ƙasar Jamus ne a cikin shekara ta 2005. Ya baro ƙasarsa ta haihuwa ne, wato Ivory Coast da ke yammacin Afirka don ya yi aiki a matsayin ɗan rawa, kuma mai koyar da raye-raye, a wani wasa da aka gabatar a duk faɗin ƙasar Jamus, wanda aka shafe shekaru uku ana yi. Bayan da kwangilarsa ta ƙare a shekara ta 2008 sai ya tare a garin Stuttgart. Ya auri wata mata 'yar ƙasar ta Jamus, kuma tun daga wannan lokaci har zuwa zancen da ake yi a yau, ba shi da niyyar barin ƙasar. Nestor ya yarda cewa

ana nuna bambanci a ƙasar Jamus sai dai kuma a nan yammacin ƙasar ana yinsa ne a kaikaice.

**Bayanin Nestor cikin Jamusanci:**

*"Nakan ji daɗin fita yawo tare da matata. Amma kuma a waɗansu wuraren hutawa da kuma gidajen cin abinci ba kasafai ake ganin 'yan Afirka ba. Don haka sai ka ga kowa ya zuba mana ido tsawon zamanmu a gurin. Suna kallonmu ne saboda sun ga na sha bambam da su, kuma ga launin jikina ya sha bambam da nasu. Abin jin daɗin dai shi ne, a nan su ba sa cin zarafin mutum kai-tsaye, amma fa suna yi da idanuwansu."*

**Mai ba da labari:**

Steve dai ya taɓa ganin wasan Nestor, amma duk da haka yana son ya ɗan kewaya don ya ga yadda gidan wasan yake. Yana sa ran ya fito a cikin wasan da ƙungiyar 'Diversité' za ta ƙaddamar, wato wasan nan na haɗakar rawar Gumboot da kuma ta Schuhplatteln nan da wata biyu masu zuwa.

**Mai gabatarwa:**

To masu saurarenmu, a nan muka kawo ƙarshen shirinmu na yau. Wannan kuma shi ne kashi na ƙarshe na shirinmu na "Ji Ka Karu" a kan mutunta al'ummomi tsirarru daga cikin al'umma. Wannan shiri dai Marta Barroso ce ta rubuta.

Idan kuna neman ƙarin bayani kan wannan shiri da ma sauran da suka gabata, sai ku ziyarci adireshinmu na yanar gizo, wato dw.de/lbe. Muna fata kun ji daɗin shirin, sai an jima.

**'Yan Wasa:**

Umma Suleiman Sagagi
Abdullahi Mohammed Kano
Fatima Abdulkadir
Abdallah Mohammed
Rabi Sufi
Rabi Salman